Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.19 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Faɗi-Tashin Auren Bahaushe: Nazari daga waƙar kassu zurmi ta shayi ɗangidan labbo

**Halima Ahmad Umar**
Tsangayar Fasaha, Shashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Jihar Sakkwato

**Corresponding Author: Halima Ahmad Umar** halimatusadiya15@gmail.com
Lambar Waya:08033527690

**Tsakure**
A kowane lokaci, mai neman nazarin wani abu na al'ada idan ya ratsi waƙoƙin baka na Hausa, yakan ji shi warkal irin na wanda ya shiga rijiya da dawonsa. Buƙatar wannan nazari ne ya dubi hoton faɗi-tashin auren Bahaushe a waƙar Makaɗa Abubakar Kasssu Zurmi wadda ya rera wa tauraronsa mai suna Shayi Ɗangidan Labbo. Nazarin ya yi ƙoƙarin dubin wasu daga cikin ayyukan da aka gudanar masu alaƙa da shi a matakan ilimi daban-daban. An yi hakan ne saboda a gano giɓin da magabata suka bari, saboda a san yadda za a cike shi. An yi ƙoƙarin yin amfani da hanyoyin tattara bayanai waɗanda suka haɗa da, sauraron waƙar Shayi Ɗangidan Labbo daga bakin wanda ya rera ta a cikin na'urar adana bayanai ta memori. Haka kuma, an yi ƙoƙarin karanta waƙar a cikin rubuce-rubucen wasu masana da suka taskance ta. Baya ga haka, binciken bai yi ƙasa a guiwa ba wajen tuntuɓar masana al'adun aure na Hausawa da kuma waɗanda suka fahimci waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi. An yi wa aikin farfajiya da waƙar Shayi Ɗangidan Labbo kaɗai, domin kada a wuce makaɗi da rawa. Wasu daga cikin sakamakon da nazarin ya bayyana sun haɗa da: Binciken ya gano yadda Makaɗi Kassu Zurmi ya fitar da wasu ɗabi'u da halaye mara kyau ga masu neman aure waɗanda idan ba a kula da su ba a wajen zaɓin miji za su zama ƙalubale ga rayuwar ma'aurata. Wannan ya tabbatar da gudummuwar da makaɗin ya bayar wajen bunƙasa al'adun Hausawa. Haka kuma, nazarin ya gano cewa, makaɗa ya yi wa iyaye hannunka-mai-sanda musamman a wajen bayar da ɗiyarsu aure don gudun kada a faɗa hannun bara-gurbi.

**Keɓaɓɓun Kalmomi:** Faɗi-tashi, Aure da kuma Bahaushe

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa:

Waƙa wata baiwa ce da Allah ya ba wa ɗan Adam wadda bai yi wa sauran dabbobi ba. Ɗan Adam kaɗai ke iya yin waƙa, domin ya shirya ta ko ya tsara ta cikin hikima da salonta da azancin ta daga ƙarshe ya aiwatar da ita kamar yadda yake son ta hau. Don haka mawaƙan baka na Hausa suka zama jagororin kiyaye al'dun Hausawa tare da rayar da su ta hanyar lugude su a cikin waƙoƙinsu. A nazarin al'ada ana nazarin matakan rayuwar ɗan Adam wato aure da haihuwa da kuma mutuwa. A cikin wannan takarda, an yi nazarin wani ɓangare ne na al'adun neman aure a cikin waƙoƙin baka waɗanda Kassu Zurmi ya gabatar. An ɗauki wasu daga cikin waƙoƙinsa ne a ka yi nazari. Duk da kasancewar waƙoƙin makaɗa Abubakar Kassu Zurmi sun fi mayar da hankali a kan rukunin maza. Wannan bai hana a iya kallato hoton wasu al'adun mutane a cikin waƙoƙinsa ba.

## 1.1 Fitilun Taken Bincike:

A wannan muhalli an waiwayi ma'anonin muhimman kalmomin da aka gina taken takardar da su. kalmomin da aka bayyana ma'anarsu su ne: Faɗi-tashi da aure da kuma Bahaushe. An yi haka ne saboda tun daga farko a gane alƙiblar da takardar ta dosa.

### 1.1.1 Faɗi-Tashi

Bargery (1993) ya bayyana ma'anar kalmar faɗi-tashi da cewa, "ƙoƙarin da mutum ke yi don samo wasu abubuwa musamman ga wanda aka ce wannan magidanci ne, ga mutumen da ke ƙarƙashinsa ko wanda bai da abin yi." Masana Harshe sun *ambaci* kalmar faɗi-tashi da jerun kalmomi ne harɗaɗu. A al'adar Bahaushe, idan aka ce faɗi-tashi kalmomi ne masu nuna jaruntaka na mutum wanda ba ya zaune ko tsaye wajen ganin ya nemi na kansa wanada hakan shi ne zai kare kansa da iyalansa daga wata barazana ta wani abu da zai illata rayuwarsa ko ya raunana mutuncinsa a kowane abu da ya shafi lamarin yau da kullum. Abin nufi a nan, tun daga aure haihuwa har mutuwa rayuwa ba ta da hutu.

### 1.1.2 Aure

Aure a rayuwar al'umma zamantakewa ce tsakanin mace da namiji wanda yake gimshiƙi ne da yake ba da cikon kamala da mutunta mutum da ba shi ragama ta ɓangarorin rayuwarsa gaba ɗaya a kowane mataki na yau da kullum. Wannan ne ya sa al'ada take mutumta duk wani jinsi na mutum da yake da aure ta ɓangarori daban-daban. Hakan ya sa namiji da mace kowane yana son ya yi aure idan suka kai matakin yin sa. Ma'ana, suka balaga kuma suka dace da abokin zamantakewa da hankali ya kwanta da shi. Idan kuma aka kalli ɓangaren addinin aure alaƙa ce da halaccin zama tsakanin miji da mata. Ana yin sa ne domin rayar da sunnar Annabi Muhammad (S.A.W) da kuma tsarkake zuri'a. Saboda haka, akwai hanyoyin da matakai da ake bi wajen neman aure waɗanda yana daga cikin abin da aka shar'anta da mutum ya yi idan har yana da lafiya da hankali da abin yin aure.

Rambo, (2013), ya ruwaito, Burgress da Locke, (1953) suna cewa: "Aure zamantakewa ce ta amincewar mutum ɗaya ko fiye da ɗaya ko mace ko fiye da ɗaya mai dangantakar mata da miji.'' Kenan a nan, aure abu ne da yake tafiya da addini da kuma al'ada. Daga cikin abin da yake kawo natsuwa ga ma'aurata akwai yarda da soyayya da hakuri da sauranasu.

### 1.1.3 Bahaushe

Sanin asalin Bahaushe wani daji ne ne mai faɗin gaske. Domin Bahaushe mutum ne mai daɗaɗɗen tarihi a doron ƙasa. Masana da dama sun ambaci haka akan wanda ya kamata a a kira Bahushe. 'Kowane tsuntsu kukan gidansu yake yi'. Adamu (1978) ya ce: "Hausawa ne daɗaɗɗun mazauna Hausa da dukkanin zuri'arsu ta fuskar maza. Ko kuma waɗanda suke amfani da al'adun Hausawa da riƙe harshensu da addininsu." Shi kuwa, Bunza (1990) ya bayyana cewa: "Hausawa dai mutane ne da suke zaune a ƙasar Hausa tun farkonta, kuma suna da zuriya a cikinta har ya zuwa yau. Kazalika, suna Magana da harshen Hausa ba su da wani Harshen in ba Hausa ba, suna da ɗabi'a da al'adu irin na Hausawa. Idan sun saɓa haka to barbarar yanyawa ne."

## 1.2 Hanyoyin Gudanar Da Bincike

Masu iya Magana sun ce: ''Kowace ƙwarya da abokiyar ɓurminta.'' Wannan bai rasa nasaba da irin fahimtar da suke da shi dangane da al'amuran rayuwar duniya, inda suka ce idan ba ka san gari ba saurari daka. Wannan ya sanya wannan takarda ta bi wasu hanyoyi farauto bayanai waɗanda suka haɗa da.

i. Sauraren waƙokin Abubakar Kassu Zurmi a na'urar adana bayanai ta memori da aka sanya wa a wayar hannu.

ii. Karatun littafin Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa wanda Magaji (2016) ya wallafa. Wannnan littafi ya ƙara wa wannnan takarada haske musamman abin da ya shafi faɗi-tashi neman aure a zamantakewa Bahaushe daga Makaɗa Kassu Zurmi. Baya ga wannan, karanta littafin ya cike wa wannan takarda giɓin da take da shi tsakanin abin da yake rubuce da kuma wanda ya rera da bakinsa.

iii. Haka kuma, an yi ƙoƙarin dubin wasu daga cikin ayyukan da aka nazarci al'adun Hausawa don sanin inda aka dosa. Wannan ɓangare ne aka yi ido biyu daga cikin wasu ayyuka. Misali, Ado, (2017) da Bunza, (2006) da sauransu.

iv. Takarda ba ta yi ƙasa a guiwa ba wajen jin ta bakin wasu masana al'ada da kuma mutanen da suke da masaniya game da waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi, inda aka yi musu tambayoyi a kan wasu daga cikin wakoƙinsa, musamman wadda wannan nazari ya tunkari lalubo wani abu na al'ada a cikinta.

v. An amfana da sauraren hirar da aka yi da Alhaji Ibrahim Muhammad (Maigirma Ɗanmadamin Birnin Magaji) a kan rayuwa da waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi. An gudanar da wannan hira a Rediyon Nijeriya na Kaduna (FRCN) a shekarar 2019.

vi. An amfana da shafin *WhatsApp* da aka buɗe saboda sanarwa wannan taro, inda masana da manazarta suka baje kolinsu da tattauna muhimman bayanai game da rayuwar da kuma waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.

## 1.3. Hanyar Ɗora Bincike

Babbar manufar ɗora aikin bincike bisa hanyar magabata ita ce, domin binciken da aka gudanar ya hau kan turba nagartacciya. Ganin cewa, wannan nazari an gudanar da shi ne omin bayyana wani abu da ya shafi al'adun Hausawa. Shi ne ya sanya aka yi tunanin ɗauko wani abu daga cikin azancinsu, domin ya zama jagora ga aikin. An yi wannan tunani ne domin a ƙara tabbatar da cewa, karen da ya yi cizo da gashinsa ake magani. Domin kuwa, bincike ne da aka gudanar da shi a kan Hausawa da al'adunsu, saboda haka ya kamata a lalubo wata falsafa ta magabata domin zama jagora ga nazarin. Sakamakon haka, wannan nazari an yi amfani da tunanin Hausawa da yake cewa: "Dukan ruwa ba zai hana gwarje amo ba." an yi wannan tunani ne domin a gwada wa al'umma irin yanayin da

Shayi yake ciki naƙamfar abin hannu bai hana shi ɗauko buƙata ba. wani abin armashi game da lamarinsa da na 'yan'uwansa, yanayin da yake ciki bai hana ɗan'uwansa tattalin abinsa ba. sakamakon zumunta yake kallo ba abin hannunsa ba, tun da ba shi da abin da zai ba shi. Duk da haka, sai ya tabbatar da abin da masu magana suke cewa: "Ɗan'uwa rabin jiki." Domin abun da ya faru gare shi, ya nuna tsananin da ɗan'adam yake ciki na yanayi, ba ya hana ɗan'uwansa ya yi tattalin abinsa, domin naka shi ne naka.

## 2.0 Yanayin Auren Bahaushe:

Tun kafin a haifi mai sabulu balbela take da farinta. Ma'ana, tun kafin Hausawa su haɗu da wata al'umma suna da al'adunsu da suke aiwatarwa a cikin mu'amalarsu. Hasali ma Hausawa suna da al'adunsu na yanayin aure da yadda ake faɗi-tashin gudanar da shi. Hakan shi ne ya sanya mai neman auren yakan bi hanyoyin neman aure kafin a ba shi mata a ƙasar Hausa. Wannan takarda ta lalabo wasu daga cikin al'adun neman aure a cikin wasu waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi da ya yi wa Shayi Ɗangidan Labbo. A nan, an fito da yadda ake neman aure a al'dar Bahaushe. Haka kuma, kasancewar mafiya yawancin Hausawa suna gudanar da rayuwarsu ne bisa koyarwar addinin Musulunci, an fito da wasu daga cikin sharuɗan aure bisa koyarwar wannan addini. Aure baya inganta sai da rukunai kamar sadaki, waliyi da kuma shaida (Muazu, 2020). Bugu da ƙari, bisa ga al'ada, idan yaro ya ga budurwar da yake so bayan sun tattauna kuma sun amince da zancen aure, shi zai tafi ya faɗa wa magabatansa ko wasu makusanta domin su sani don ɗaukar matakan da suka dace. Sannan a bi matakan da al'ada ta tsara don cimma manufar abin da aka dosa.

## 2.1 Neman Aure

Hausawa sukan ce:''Ba neman aure yake da wuya ba, shiga ka fito''. Wannan karin magana yana nuna cewa, neman aure ya ƙunshi hidimomi masu yawan gaske. Yanayin aure yakan fara ne daga lokacin da saurayi ya isa aure (balaga). Shawarwarin iyaye tare da na 'yan 'uwa da abokan arziki sun atimakawa lamarin ta fuskar armashi da samun karɓuwa.

Daga nan ne soyayya takan ƙullu a tsakanin saurayi da kuma budurwa da yake nema ya aura. A bisa kowane zance dai aure ba ya samuwa ba tare da an nema ba. Da zarar yaro ya isa aure haƙƙin iyayensa ko danginsa ne su nemo masa mata da ta dace da shi, ko kuma kamar yadda muka faɗa a baya wato idan Allah ya sa ya ga wadda ta kwanta masa a rai sai ya faɗa da kansa. Ya nemi hanyar magan da ita ko hanyar yi mata ɗan kyauta don ta fahimce shi ko kuma ya gaya mata kai tsaye ko abokansa su sanar da ita.

Wannan yake sa idan suka fahimci juna iyaye za su shigo inda za su kai sallama ko gaisuwa a gidan iyayen yarinya daga ƙarshe a sami lokacin da za a saka rana aure da kuma sauran kyayyakin da al'ada ta tanda don auren ya yi armsahi tare da yin shagulgulan buki. Saurayi zai ci gaba da zuwa gidan su yarinya yana yi mata kyauta ko toshi kamin wannan rana da aka saka ta auren. Kyauta tana ɗaya daga cikin abin da ke ƙara dangon ƙauna da soyayya a cikin neman auren Hausawa. Akan samu aure da yawa ya faɗa cikin tangarɗa idan wanda yake neman auren ba ya da kyauta. Wannan ya sa Kassu Zurmi a ɗangon waƙarsa da ya yi wa Shayi ɗan gidan Labbo ya kira shi da ɗangoshi. Ma'ana, marar sa'a tun da ba ya yin kyauta ga 'yan matan da ke son sa. Ga abin da yake cewa:

Jagora :Ku hwalka na kai ga masu ɗongashi,
: Lalle Sha-yaya ad da ɗangashi,
:Ya yi biɗa amre bara sai da yas samu,
:Ya kai ta gidan maigidansu yah hwaɗi,

:Yam mutu yab bas shi ba a bin amren,
:Kana ba hatcin ɗiba.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Makaɗa Kassu ya nuna Shayi ya nemi aure in da a al'adar Bahaushe ana kai mace gidan saruki don a gan ta ko ta gaishe su. Wannan ya sa Kassu ya nuna cewa mahaifin Shayi ke ba shi kuɗin neman auren ga shi ya mutu. Kuma ba ya ga wannan, ya yi rashin mai ciyar da shi. Abu na biyu ya sami matar , amma ga shi ba hatcin ɗiba. Ma'ana ba abinci.

**2.2 Kalubale ga Mai Neman Aure**

Wannan kalma daga Harshen Larabci aka aro ta. Hausawa suna amfani da ita domin ta maye masu gurbi da wasu matsaloli da suka yi masu yawa a cikin rayuwarsu ta neman aure. A kowane al'amari na rayuwa, za a tarar akwai jarabobi da suka tattara ga rayuwar mutum. Don haka dole ya zamo mai ɗaukar ƙaddara mai kyau da kuma akasin haka. Masu hikima suna ganin duk auren da ba a sami ƙalubale a cikinsa ba a ji tsoronsa. Wannan ya sa yana daga cikin matakan da mai neman aure zai yi tarayya da wannan ƙalubale. A al'adar Bahaushe ba a bayar da aure ga wanda ba shi wata sana'a da ya dogara da ita. Bahaushe ya tashi ya sami kansa da iyayensa da kakaninss mutane ne masu dogaro da kansu ba cima kwance ne ba. Wannan ya sa a gidan Bahaushe za a tarar ya ɗauki sana'a da muhummanci a rayuwarsa. Babban ƙalubalen ga mai neman auren ya zamanto ba shi da sana'a. Wannan dalili ya sa Makaɗa Kassu Zurmi yake cewa:

Jagora : Kakab bana tai kyawo,
: Ko ta bara mun gode,
: Sai dai sha- yaya bai yi komai ba,
: Naga 'yan tantabaru cikin *ruhewassu.*
:Tantabara goma,
: Amma yanzu basu sun ƙare,
: Yanzu kam saura nai guda baƙi namiji,
: Ko shi kam dan yana yi mai waƙa,
: Inda sahiya taw waye ya ɗora mabanci.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Wannan ya sa Kassu Zurmi ya nuna ubangidansa da ya yi noma a gonarsa wanda jama'a suke wadata da shi, amma shi ubangidansa bai sami komai ba. Hasali ma a cikin ruhewarsa (rumbu) inda ake ajiye amfanin gona babu komai sai tantabaru. Ya nuna babu hatsi a ciki, su ma tantabarun sun ƙare saura guda ɗaya, bai taƙama da komai sai talauci. Kassu ya ƙara da cewa:

Jagora : Tantabar na riga ka tasowa,
: Kai ga ka da ranka kwana sai luhwa ta shuɗe,
: Sai tsuntsu ya hito yana shan hantci,
: Yana gashin ƙeya,
: Shina dubin inda za ka hudowa,
: Shi kau yana cikin ɗaki,
: Tantabara na gyaran jiki nai,
: Sai da Shayi-yaya yaɗɗago ɗaki,
: Dam mazan tantabarin ga na yi mai guɗa,
: Shina ƙudunguru Shayi ɗan gidan Labbo,
: Kudunguru Shayi ɗan gidan Labbo,
: Kudunguru Shayi ɗan gidan Labbo,

: Shi ko ko kirzon,
: Shi ko ko kirzon sai ya watsa yas tsaba sai ya watsa yats tsaba,
: Kai ko tsuntsu tcintace tciyakku ta bi ku,
: Kai ko tsuntsu tcintace tciyakku ta bi ku.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

A al' ádar Bahaushe ba mai son a ce surikinsa rago ne wanda bai iya neman na kansa yana kwance sai dai a samo a ba shi. Wannan ƙalubale ne ga iyayen yaro da ya tashi bai iya neman na kansa sai an ciyar da shi balle matar da za ta rayu tare da shi da 'ya'yansa. Wannan ɗango, Kassu ya nuna Shayi rago ne malalaci mai mutuwar zuciya ya haifar masa da bai iya tashi ya biɗi na kansa. Balle har ya nemi abin da zai ciyar da matarsa da yake nema. Haka kuma, a tsarin na gidan Bahaushe mutum ne mai yin sammako don zuwa gona ko wasu sana'o'i masu muhimmanci a rayuwarsa. Makaɗa Kassu ya ambaci da Shayi saboda rangancinsa sai rana ta fito yake tashi daga baccin safe. Shi ma tashin nasa, sai in wannan tsuntsun da ya rage masa a ruhewa ya tada shi domin ya ba shi naa kallaci sai watsa masa hatsi. Wannan yana daga cikin sharuɗan da ba za a bai wa mai neman aure yarinya ba idan har bai da sana'a wadda ya dogara da ita. A Musulunci shari'ah ta yi hani a ba mutum aure idan ba shi da abin yi, ma'ana bai da sana'a r da ya dogara da ita. Bugu da ƙari, Hausawa mutane ne da suke kallon hoton halayya da ɗabi'a kyawawa na al'ummarsu. Wannan ya sa yana daga cikin sharuɗan neman aure a kalli ɗabi'u masu kyau da akasin haka kamin a ba da aure ga mutum. Idan mu ka kalli yadda Makaɗa Kassu ya ba da labarin yanayin ɗabi'ar Shayi ɗan gidan Labbo akwai darasi a cikinta.

Jagora : Labbo yac ce ƙaton gidan banza ne,
: Komi yab biɗa na mata ne,
: Dum mata sun bi Iro sun koɗe,
: Yaƙ ƙamnatai tana yi mai wazu,
: La'anannen ba ya jin batun ƙamnai,
: La'anannen ba ya jin ba,
: Tana hwaɗin,
: Tana hwaɗin Shayi ga ka dai da ƙarhinka,
: Shayi ga ka dai danka,
: Na Abu hak ka lalace tsohuwa ta cishe ka,
: Na Abu hak ka lalace tsohuwa ka cishe ka.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Wannan wani ƙalubale ne ga mai neman aure a same shi da wata ɗabi'a ko hali marar kyau wanda zai iya zama tarnaƙi a hana masa aure. Kassu ya kira Shayi ƙaton banza wanda bai da wata moriya. Kazalika, ya siffanta Shayi da manemin mata, wanda duk abin da ya tara mata ne suke amshewa ba wai da sunan auren ba kawai, a banza da wofi suke karɓa. Baya ga wannan, ɗabi'ar da ke ga tattare da Shayi ta saɓawa wa tarbiyya a al'adar Bahaushe. Domin ƙin sauraren maganar iyaye da dangi da kuma al'ummar gari kure ne babba. Haka ma, an san ɗiyan Hausawa da tausayin iyaye musamman tsofaffi, amma Kassu ya labartawa masu saurare Shayi ayan rasuwar mahaifinsa Kakarsa ta Uba ce take ciyar da shi, maimakon shi ya dace ya kula da ita. Son holewa da hutu shi ne ya jawo ya kasa ci da kansa, sai kakarsa ce take ciyar da shi. Daga ƙarshe ya nuna a yi masa nasiha ko zai gyaru daga halayyarsa maras kyau.

### 2.2.1 Soyayya

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

Hausawa sukan ce: ''So hana ganin laifi." So a zuci yake nan ne tushensa, nan ne turkensa, duk wurin da ya je yawo ya dawo a nan (Bunza, 2006). Wasu iyaye sukan bar 'ya'yansu mata su je wajen buki ko gidajen 'yan'uwa ta nan ne suke haɗuwa da samari. Haka ma, wasu 'yan matan sukan je dandali domin yin wasa da sauran abokansu ko kuma wajen kallon wasannin gargajiya inda ta nan ne suke haɗuwa da samari ko mazajen aurensu. A irin waɗannan wurare ne akasarin 'yan mata ake masu tayi ko kyauta da manufar nuna ƙauna irin ta neman aurensu. Wannan ya sa wasu mazan kafin su je irin waɗannan wurare sukan yi kwaliya domin su burge 'yan matan da suke cikin wannan dandali.

Jagora : 'Yammata sun gane shi sun je mai,
: Anka ɗora wasoso,
: Ni wanin Shayi ni ka jiɗe shi,
: A'a kina ƙarya na riga ki zaɓo shi,
: Kamas su buga ga su nan cikin *gebe*,
: Na ce kak ku buga ya ishe ku jiɗawwa,
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Kyau yana daga cikin abin da mata suke kallo su nuna soyayyar su ga fili ga mai neman auren su. Kuma yana daga cikin abu mafi muhimmanci a wurin akasarin mata a wajen zaɓen miji. Sakamakon haka, dogon bakin Shayi da kuma kyawon yankan bakinsa da tsayinsa suna daga cikin abin da ya tattara hankulan 'yan mata har ya sami soyuwa a wajensa. Wannan kuma har yanzu mata sun fi son mazan da suke da siffar kyau fiye da waɗanda suka kasance akasin haka.

### 2.2.2 Kiyayya

So da ƙi duk gurbi ɗaya suke a ƙoƙon zuciyar ɗan Adam. Idan ƙiyayya ta tsananta takan sa a yi mafarkin abin ƙi, wasu lokuta a yi mafarkin an ci galaba a kansa, a wani lokaci kuwa a yi mafarkin ya ci galaba a kai (Bunza, 2006). Kishiyar soyayya ita ce ƙiyayya, musamman idan abin da ake so a rasa shi ko kuma akasin haka. Wannan ya sa rashin gaskiya da amana a wajen neman auren Bahaushe yakan haifar da ƙiyayya a tsakanin masoya da dama. Haka kuma, akan samu rashin jituwa wadda take wanzar da ƙiyayya idan wanda yake nema ya zama mutun ne marar kyauta da kyautawa a tsakanin mosoya. Waɗannan halaye suna daga cikin abin da ya jawo ma Shayi rashin yarda a tsakanin shi da 'yanmatan da suka ba shi masauki kamar yadda Makaɗa Kassu ya fito da hoton abin da ya auku inda yake cewa:

Jagora : Sai da za mu watcikewa
: Sannan uwayen matanga sunka jawo ni
: Ga ni ga 'yanmatan ga, ga uwayensu
: Mu kaɗai cikin zaure,
: " Kassu amana 'Allah kaba mu labarai,"
: Nic ce wane labara,
: "Labarin Shayi ɗan gidan Labbo,
: 'Yanmatan sun walwale baikonsu,
: Sun ce Shayaya shi ka ramkon su,
: Shi muke son kaba labara,
: In akwai gidan kirki."
: Nic ce yau kau dattijo kunka mai she ni,
: Yaya, ku kuma shaida? Na-Abu ɗan 'uwana ne,
: Yaya. Ku kuma shaida? Na-Abu ɗan' uwane ne,

: Mutum ƙau ba ya shaidaɗ ɗan 'uwansa ko hwaɗa.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Yaba kyauta tukuici in ji Hausawa. Wannan yana daga cikin abin da ya ƙara ba iyayen 'yanmatan nan tsoro, wanda hakan ba al'adar Bahaushe ba ce. Hakan ya sa suke tantama game da Shayi don su tambayi ubangidansa ya faɗa musu gaskiyar halayarsa. Domin kuwa a ƙa'idar neman aure ba za zartar da shi ba sai dattijai sun yi bincike game ɗabi'ar wanda za a ba. wannan ya haɗa da yanayin gidansu da kuma sana'ar da ya dogara da ita. Kassu ya faɗi yadda ta kaya tsakaninsa da uwayen 'yanmata kamar haka:

Jagora : "Kassu amana 'Allah ka ba mu labari,
: Ni kau amana Allah kaɗai ka sha min kai,
: In na bi amana 'Allah na yi ɓatanci,
: Kuma in na tuna ba ni cin amana 'Allah saboda tantiri,
: Na –Abu Shayi dai ɗa ne,
: Sunka ce "Ba haka munka so ba ɗan yaro,
: Ba mu labari in akwai gidan kirki,
: Ai mun san ɗa ne tun da anka haihe shi.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

A tsarin Hausawa, idan za a yi baiko ga mai neman aure abu ne mai wahala a yi ba tare da an yi bincike ba. Dattijai ne a kan gaba wajen binciko wanda yake neman aure. A nan ne za a binciko nau'in gidan da ya ffito (na dattako ne ko akasinsa) da danginsa da kauma abokansa da yake hulɗa da su. A muhali na bincike yakan faɗa ga wanda ga ɗan'uwansa da abokinsa har ma maƙwabata ake tamabaya halayen mai neman aure. Aure abu ne da ake son idan za a yi shi babu ɓoye-ɓoyen kowane aibu daga cikin dukkaninsu ɗayan biyu ne, wato mata da miji. Saboda gudun can gaba kada ya haifar da wata matsala. Amma a tsari irin na zamantakewa yana da wahala ɗan'uwa ko aboki ya faɗi ɗabi'u marar kyau na ɗan'uwansa musamman a sha'anin aure. Yana daga cikin abin da yake sa wasu ba su bincike ta hannun ɗan'uwan mai neman aure. Duk da haka da suka danganta Kassu da mahalicinsa ya rike amana.Wannan ya sa Kassu ya ji tsoron Allah ya yi masu hannunka mai-sanda duk da yake ɗan'uwan Shayi ne amma bai hana shi faɗin gaskiya halinsa. Duka wannan hoton ɗabi'un mutane makaɗa yake fayyacewa ba halin Shayi ne haka ba.

'Yan mata sun buƙaci Kassu ya gaya musu gaskiyar cewa, wane ne Shayi, Kuma ya halayarsa take? Wannan halaye na Shayi da Kassu Zurmi ya labartawa uwayen 'yanmatan nan babu hali ɗaya na ɗauka. Wannan ya sa dattijo ya yi fushi ya hasala, ya bar su Kassu nan zaune ya wuce abinsa kamar yadda Makaɗa Kassu yake cewa:

Jagora : Dattijo yat tashi,
: Yab buge rigar yai cikin zaure.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

### 2.2.3 Fafutukar Neman Abin Shagalin Biki

Al'adar Hausawa idan lokacin aure ya taso mai neman aure yakan kai ya dawo don fafutar ganin ya yi ƙoƙarin yin duk wasu abubuwa da suka shafi shagalin buki. Wannanya haɗa tun daga kan ɗawainiyar da take kan amarya har zuwa danginta wanda ta haɗa da kuɗin da za a kashe da abinci da za a ci a wajen shagalin buki da tarbon baƙi da wasanin da za a gudanar da sauran su. Akan yi iya gwargwado ganin ba a ba maraɗa kunya ba. Wannan yana daga cikin abin da yake faranta zuciyar masoya musamman waɗanda aka yi abin dominsu. Ga yadda Kassu yake labartawa al'umma hoton abin.

Jagora : Don an game da Labbo yana tattalin ɗiyan dangi,

: To daɗa ra amren Sha, Labbo ya wahala,
: Ra amren Sha, Labbo yai yawo,
: Yai yawo,
: Amren Sha-yaya, Labbo ya yi jidali.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

A wannan ɗango za mu ga cewa, Kassu ya nuna irin fafutukar da Shayi ya yi da wahalar yawo da kai da kawo da yake na ganin cewa ya samu abin yi lalurar shagalin buki. Duk da haka albasa ba ta cimma ruwa. Baya ga wannan, Kassu ya bayyana cewa bayan wahalhalun da Shayi ya sha na jidali da kai da kawo ya sake shawara don ya canza tun da bai sami ba, bari ya je ya nemi bashi wataƙila ko za a dace. Makaɗa Kassu ya larabata mana cewa:

Jagora : Garin biɗaɗ bashi.
: Ya sha raba kamak Karen daji,
: Ya sha rana kamat tuƙin ɗaki,
: Labbo ya tawaiwaye walki shina ginah hanya
: Maidabo ɗan auta za ya ba shi yah hwasa.
Jagora : Irin gidan bawa ɗan galadima,
: Sai da bawa yab bashi sai Taɗari taƙƙwace,
: Tac ce sabilin Sha-yaya ba a bashe su,
: Ɗan nema bai raga ma kowa ba,
: Wata yag gona garai cikin tabki,
: Bara yat tashi yana kashin awakinmu,
: Tac ce masalin mai ƙato gudan awa Shayi,
: An nan ka biɗab bashi.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

A ganin Gobir, (2020) bashi shi ne, "karɓar wani abu musamman kuɗi da niyyar biya ko mayarwa bayan wani lokaci. Ga al'adar Hausawa idan lokacin buki ya zo an aro bashi domin a yi wasu sauran lalurar shagalin buki domin, idan danbu ya yi yawa ba ya jin mai. Wannan yake sa idan an gama shagali hankali ya kwanta akan mayar wa mai kuɗi abinsa. Duk wanda ya yarda da kai ya ba ka bashi, to ya kyauta maka. Idan ya hana ka to lalle dangantaka takan yi tsami a tsakaninku. Kassu ya bayyana cewa, Shayi ya yi ta zuwa wurin dangi da sunan neman bashi ga mutane bai samu ba. Wannan ya nuna Sahayi ba ya da alfarma da za a ba shi ko da aro ne. Sakamakon bai da sana'a da ya dogara da ita balle a yi tsamnin ya biya bashin da ya karɓa daga baya.

### 2.2.4 Zumuntar 'Yan'uwa Kan Lamarin Auren Ɗan'uwa

Zumunta a ƙafa take in ji Hausawa! Zumunci shi ne dangantaka ko nasaba ta jinin ko ta soyayya ko ta maƙwabtaka, watau ta zaman tare. Bahaushe ya ɗauki zumunci da muhimmanci, don haka ne za ka samu yana kwaɗaitar da yaransa da yin zumunci ta hanyar ziyara, da auratayya (Mu'azu, 2020). Zumuntar 'yan'uwa aba ce wadda take ɗaukar ragama na farin ciki da kuma akasin haka. Irin wannan dangataka ta jini ce ta sa dangin Shayi suke ta takalihu da shi duk da yake bai tashi ya nemi na kansa kuma ya raina sana'a da tashi a cikin wadda ya gada kaka da kakanni ba. Hakan ya haifar wa danginsa yin takalihu shi da ɗawainiyarsa musamman ta ciyar da shi da kuma ba shi kuɗin neman aure da na neman mata. Makaɗa Kassu ya faɗa a ɗiyan waƙarsa inda yake cewa:

Jagora : Ta Ɗangiwa Hauwa na yi mai biɗa,
: Ba ta da ƙarhi ba ta biyak kuyya,

: Yat tahwasa taka ɗiba a ba ta sadare,
: Ta kau ci hat ta cishe shi,
: Taro kun san ko ha uwa uba nai ce.
Jagora : Katakoran Lando, Iro na Ummaru,
: Kura mai guzurin kunya,
: Sha-yaya Magarya ta yi ma doro,
: Tana nan ta bar ka, Atu ta tcere,
: Dauri an bar maka tsohuwa ta cishe ka,
: Tsohuwag ga ta tuzge,
: To daɗa Sha wa ka cishe ka?
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Al'adar Hausawa idan tsofaffi suka gaza saboda ƙarewar ƙarfi, akan dubi bayansu ne da suka bari, ma'ana haihuwa da suka yi za ta yi amfani. Domin su ne a lokacin ragamar gidan za ta koma kansu na ɗaukar nauyin iyayensu da kakaninsu da duk wata ɗawainiyar gidan. Kassu ya gaya mana a wurin Shayi ba haka ba ne, saboda ubansa ne yake ɗauke da nauyinsa da kuɗin neman auren da yake ba shi kamar yadda aka ambata a baya. Bayan da ya rasu, sai ragwamar Shayi ta dawo hannun kakarsa ta Uba, ita ke biɗa tana ba shi da 'yan sana'o'inta na gida. Daga ƙarshe ita ma ta rasu aka bar Shayi shi kaɗai. Wannan ya nuna mana irin ƙarfin zumuntar Hausawa. Koda kowa zai guje ka, danginka na jini ba za su guje ka ba.

### 3.1 Gudunmawa

Zamantakewar Hausawa tana da tsari irin na Hausawa cuɗe-ni- in-cuɗe-ka. Wannan ya sa suke haɗuwa a kowane al'amari na rayuwa suke taimakon junansu ko su haɗa kafaɗa da kafaɗa don kawo gudummuwa domin magance wata matsala da ta shafi marasa ƙarfi a cikin su. Abin da ya shafi ciwo, da aure da haihuwa da noma da taimakon gaya a cikin 'yan uwa da abokan araziki. Hausawa sukan taka muhimmiyar rawa a wajen ba da tasu gudummuwa idan wani daga cikin iyalansu suka shiga hidimar ɗaura aure ko ta haihuwa. Ba wai mata kaɗai ba, har da maza suna ba da tasu gudummuwar don ganin an rufa wa juna asiri tsakanin 'yan'uwa. Wannan a wajen Bahaushe yana da wuya ya zo wajen lalurar bukin aure ba tare da ya zo da tashi gudummuwa ba. Ko da daga gari mai nisa ya zo zai riƙo wata tasa gudummuwa domin a ga cewa an fita kunyar jama'a. Duk da Kassu ya nuna Shayi bai samu ɗaya daga cikin wannan gudummuwa ba a dalilin wasu ɗabi'unsa, da rashin gudanar da wata sana'a da kuma rashin tausayinsa da lalacisa da kuma son hutunsa.

Jagora : Labbo yac ce ƙaton gidan banza ne,
: Komi yab biɗa na mata ne,
: Dum mata sun bi Iro sun koɗe,
: Yaƙƙamnatai tana yi mai wazu,
: La'anannen bay a jin batun ƙamnai,
: Lla'anannen ba ya jin ba,
: Tana hwaɗin,
: Tana hwaɗShayi ga ka dai da ƙarhin,
: Shayi ga ka dai danka,
: Na Abu hak ka lalace tsohuwa ta cishe ka,
: Na Abu hak ka lalace tsohuwa ka cisheka.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

### 3.1.1 Sutura

Sutura tana daga cikin abin da yake ƙara saka wa mutum ƙwarjini da ƙara masa ƙyau a jikinsa. Hakan yana haifar da Shayi wannan kwarjini a idon 'yanmata. Ganin irin kayansa na alfarma ya sa suka raja'a a kan Shayi. Akasarin mata suna zaɓen namiji a lokacin da suka gan shi yana sanaye da sutura mai tsada. Musamman idan baƙo ne ya zo daga nesa. Ganin wannan sutura ta Shayi ya sa 'yanmata da dama suke ta gaggawar ganin kowace ta samu shiga a wurinsa. A tunaninsu mai abin hanunsa ne. Makaɗa Kassu yana cewa:

Jagora : Wasan da munka zo tare da 'yan Magarya,
: Tai kyawo,
: Rannan Sha-yaya yas shigo sa'a,
: Ga ya da dogon baki da 'yaw wutab ɓota,
: N a Abu yankan bakinka ya yi ma kyawo,
: Ya samu gama aron zanen saƙi,
: Had da *tsamiya* yaɗɗauro da yab baƙas *shadda*,
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Shigar da Shayi ya yi ta ƙayatar da 'yanmata, shi ya sa 'yanmatan suke son sa har suka yi jayayya a tsakaninsu. Kowace tana son ya sauka a wurinta a matsayin baƙonta kuma saurayin da za ta zaɓa don shi take muradin aura. Daga ƙarshe suka aminta suka sauke shi su dukansu suka zaɓi ɗaya daga cikinsu ta zama mai masaukin baƙi, kowace ta tafi ta haɗo abinci mai kyau domin ta shiga gasa, wataƙila ko za ta dace Shayi ya zan matsayin uban 'ya'yanta.

### 3.1.2 Abinci:

Bisa ga al'ada, masoya saurayi da budurwa da suke ƙaunar junansu da niyar ƙulla aure a tsakaninsu sukan kyautata wa juna ta hanyar toshi. A tsarin wannan al'ada, namiji ne yake ba mace toshi. To amma ita mace tana da tata kyautatawa da take yi wa masoyinta, musamman lokacin da ya baƙunce ta. Idan ba a gari ɗaya suke ba. Hanyar ba shi ɗan abin da ya sawaƙa daga cikin abin sana'arta irin wannan ya sa Abubkar Kassu Zurmi ya labarta a cikin waƙarsa inda yake cewa:

Jagora : Ɗaukash Sha-yaya munka sha daula,
: Mun sha ɗamnalutsa mun sha mai,
: Mun sha zabbi ga ɗan gidan Labbo,
: Nic ce ma 'yan yarana, ku sha ahaha ce,
: Tun da ba ya maishe ta.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Idan mu ka kalli wannan ɗango, yana nuna tabbas 'yanmatan da suka sauke Shayi sun karama shi da abinci tare da makaɗinsa Kassu Zurmi. Sun ba su soyayyun 'yan shila da man shanu da soyayyen naman zabi. A al'dar Hausawa, idan 'yanmata suka yi wa saurayi irin wannan saukarwa, idan ya tashi tafiya zai yi musu kyautar kuɗi waɗanda suka fi abin da suka kashe wajen sayen kayan abincin nan. Daga kyautar ce ake gane yanayin yadda zaman auren zai kasanace. Saboda halin tsiya da Shayi ke da shi. Kassu ya ba su umurni ya nuna musu cewa, asara ce kawai 'yanmatan nan suka yi domin Shayi dai ba shi da abin da zai baya su. Don haka sun ci ahaha.

## 4.0 Ɗaukar Takalihu Bayan Aure

Baya ga gudummuwar 'yan'uwa da baokanin arziki da fafutukar neman shagugulan buki da aka yi wa mai aure akwai sauran rina a kaba. A yanzu ne mai auren ragama za ta dawo kansa na duk wani motsi a cikin gidan. Bahaushe mutum ne mai kai da kawo ganin ya nemi abin da zai ɗauki takalihu iyalansa na ci da sha da sutura da muhali da ciwo. Idan kuma an sami ƙaruwa nan ma wani ƙarin takalihu ya ƙaru. Domin da uwa da ɗiyan duk shike da hakin yi musu ɗawainiya har sai lokacin da yaran suka kai wani mataki na rayuwa. A lokacin shi ma zai ɗan sarara, amma duk da haka yana ba da wata gudummuwa da yake bayarwa matuƙar zai iya fita ya je ya dawo kuma yana da lafiya. Da yawa za ka samu tsofafi da dama ga su sun kai shekaru aru-aru. Wannan bai hana su zuwa zagaye na gonakinsu don yin noma da sauran cin kasuwanni daga wannan gari zuwa wancan. Wannan bai rasa nasaba da dama, Bahaushe mutum ne mai faɗi-tashin ganin ya kare wa kansa daga cuta talauci da kuma roƙo. Kassu Zurmi ya faɗa da uwayen 'yanmata cewa, Shayi bai iya ɗaukar takalihun mata sai dai in ita matar za ta ɗauki nauyin ci da kanta ga yadda ya ce:

Jagora : Nic ce I, gaskiyarka dattijo,
: Mutum kau ba za ya kai ɗiyatai ba,
: Gidan da ba abin kirki,
: Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,
: Sai ɗiyat dattijai kaɗai ka amren,
: Shayaya ɗan gidan Labbo Na-Abu,
: Tun da kowa amre shi ita ka ci she shi,
: Ta biya kuɗin garin karen kyasko,
: Sannan ta yi mai abin ruhwa
: Kana ta koma ta yi dabbalin abin ɗamri.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Babu mai son ya kai akuya tai kasuwa ta dawo tana ci masa danga. Wannan ya sa dittjai da iyayen 'yan mata suka watse don suna ganin kamar ɗiyansu za su faɗa cikin wahala. A al'adar Hausawa komawa bayane da namiji mace ta ɗauki ragamar gidansa, amma kuma wasu na ganin kamar dace wace a ce ka sami mace da take ɗaukar ɗawainiya gida ga yadda wani Makaɗi ya ce: Wani gwarzo na, Barani, Auren Barai, kuma irin abin nema ne da Hausawa suka cewa: ''Allah ya yi aure da marar kwabo."

Jagora : Barau Allah yayi ma rabo,
: Yay ma babban Arzikin,
: Tun da yay maka mata zaruma,
: Hura cike ba ta hatcinka ba,
: Ka ci tuwo da miya sai ka kaji.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Maimakon ya ciyar da matar ita ke ciyar da shi yana can wajen neman magungunan tauri. Bayan ci da kanta kuma ta yi mai tufafin sakawa, sannan ta yi wa kanta. Wannan ya nuna Shayi ya kai iyakar malalaci.

## 5.0 Sakamakon Bincike

Sakamakon bincike wasu abubuwa ne da ake ganowa bayan an kamala binciken da aka gudanar. Daga cikin abubuwan da wannan takarda ta kai ganowa akwai:

i. Dawo da tarbiyar al'umma irin yadda magabata suka yi a baya. Hakan zai sanya kowane yaro ya zama dole ya koyi sana'ar gidansu koda kuwa zai iya wasu sana'o'in daga baya.

ii. Rage dogaro da gwamnati kamar yadda magabatanmu suka yi a baya.
iii. Binciken ya gano yadda Makaɗa Kassu Zurmi ya fitar da wasu ɗabi'u da halaye marasa kyau ga masu neman aure. Waɗanda kuma idan ba a kula da su ba a wajen zaɓin miji za su zama ƙalubale ga rayuwar ma'aurata. Wannan ya tabbatar da gudummuwar da makaɗin ya bayar wajen bunƙasa al'adun Hausawa.
iv. Binciken ya hankaltar da iyaye musamman a wajen bincike na bayar da ɗiyan aure da su kula sosai don gudun kar a faɗa ga hannun bara gurbi.
v. Binciken ya gano yadda Hausawa suka darajanta sana'o'insu na gargajiya, kuma shi ya sa ake yawan jin ana faɗin su a cikin maganganunsu yau da kullum.

**5.1 Kammalawa**

Wannan takarda ta dubi faɗi-tashin Auren Bahaushe: Nazari daga waƙar Makaɗa Kassu Zurmi ta Shayi ɗan gidan Labbo. Za a iya cewa, "haankali ne da kaya ya fi ban cigiya". An faɗi irin faɗi-tashin da Shayi ya yi da ƙalubalen da ya sha da wahalhalun da ya faɗa na neman taimakon 'yan'uwa da abokanin arziki saboda haƙarsa ta cimma ruwa a wajen neman aure. Duk da haka, sakamakon rashin sana'a buƙata ba ta biya ba. Wannan tunani da fasaha da Kassu ya fitar da su a cikin hoton rayuwar al'dun Hausawa ya zama madubi ne da zai ƙara haskaka rayuwar al'ummar Hausawa.

**Manazarta**


Ado, A. (2017). *Ra'o'in Bincike kan Al'adun Hausawa.* Katsina: Kanki Classical Media Enterprises.

Alhasan, H., Musa,U.I. da Zarruƙ,R.M. (1982). *Zaman Hausawa Bugu Na Biyu*. Lagos: Islamic Publication Bureau.

Bunza, A.M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Publications Limited.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya (2006). *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zariya: Ahmadu Bello University Press.

Halima, A.U. (2016). Sunayen Bahaushe a Idon Maƙwabtansa. Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Magaji, M.G. (2024). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa.* Ibadan: Spectrum Books Limited.

Mu'azu, S.M. (2020). *Bahaushiyar Al'ada.* Kano: Bayero University Press.

Maikwari, H.U. (2021). Nason wasu Al'adun Hausawa A tunanin Marubuta waƙoƙin Hausa. Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Rimmer E.M. da Wasu. (1966). *Zaman Mutum da Sana'arsa*. Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Sa'idu, M.G. (1996). *Makaɗa Da Mawaƙan Hausa.* Kaduna: Ɗab'in Fisbas Media Services.

Saulawa, I.A (1986). Yanayin da Tasirin Al'adun Aure a Kasar Katsina. Sakkwato: Kundin Digiri na Farko. Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Yahya, A.B. (2016). *Salo Asirin Waƙa.* Kaduna: Ɗab'in Fisbsas